Allah - Maɗaukakin sarki - Ya ce: Mutum uku zan yi rigirma da su a ranar alƙiyama

Daga Abu Huraira - Allah Ya yarda da shi - daga Annbai - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: "Allah - Maɗaukakin sarki - Ya ce: Mutum uku zan yi rigirma da su a ranar alƙiyama: Mutumin da ya bada amana da sunana sannan ya yi yaudara, da mutumin da ya saida ɗa ya ci kuɗinsa, da mutumin da ya hayi ɗan ƙodago ya cika masa aikinsa amma bai ba shi ladansa ba".

[Ingantacce ne] [Bukhari ne ya rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya bada labarin cewa Allah - Maɗaukakin sarki - Ya ce: Nau'i uku na mutane zan yi rigima da su a ranar alƙiyama, duk wanda na zama abokin rigimarsa kuwa zan rinjaye shi: Na farko: Wanda ya rantse da Allah, ya yi alƙawari. sannan ya warware shi ya yi yaudara. Na biyu: Wanda ya saida ɗa akan cewa bawa ne, sai kuma ya ci kuɗinsa ya yi tasarrufi da ƙimarsa. Na uku: Wanda ya dauki ɗan ƙodago dan yin wani aiki, sai ya kammala masa aikin, amma bai biya shi kuɗin aikinsa ba.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/66163